RESOLVE NETWORK

TAKARDAR BINCIKE

# MAKIYAYA DA ZAMAN LAFIYA NA YAU DA KULLUM:

## MUHIMMAN HANYOYI DA DARUSSAN WANZAR DA ZAMAN LAFIYA DA YAYYAFAWA RIKICI RUWA DAGA TURKANA TA AREWA TA KASAR KENYA

Wannan takarda na ɗauke da sakamakon binciken da ƙungiyar RESOLVE ta gabatar, « na Makiyaya da Zaman Lafiya Na Yau da Kullum: Muhimman Hanyoyi da Darassu Domin Wanzar da Zaman Lafiya da Yayyafawa Rikici Ruwa daga Turkana ta Arewa a ƙasar Kenya,» daga Caleb Maikuma Wafula. An shafe shekara ashirin, ana tattaunawa da yin muhawara a duk faɗin duniya kan cewa yana tsarin makiyaya da al’asunsu da yanayin tattalin arzikinsu shi ne musabbabin yaduwar rikice-rikice a faɗin yankin Afirika. Makiyaya suna fuskantar matsin tattalin arziki, da muhalli, da zamantakewa da siyasa. A sakamakon haka, yan siyasa da jami’an tsaro suke ɗauka makiyaya a matsayin masu tayar da ƙayar baya, masu barazana ga zaman lafiya da doka a wuaren da suke zaune. Wannan abun ne da ke zahiri kuma ya sa an manta da irin gudummuwa da makiyaya ke bayarwa wajen tabbatar da cigaba mai ɗorewa, da rawar da al’ummar makiyaya ke takawa a yankunansu wajen wanzar da zaman lafiya da tabbatar da cigaba a karkara da alƙaryu da ƙasa baki ɗaya. Wannan sakamakon bincike da aka yi amfani da dabarun bincike mabambanta, binciken ya gano hanyoyi da dabarun gargajiya na wanzar da zaman lafiya da yayyafawa rikici ruwa a al’ummar makiyaya mazauna yankunan Turkana a ƙasar Kenya tare da matsaloli da ƙalubalen da suke fuskanta. Darussan da suke ƙunshe cikin wannan binciken za su taimaka mana wajen fahimtar yadda hukumomi da masana za su iya tunkara da magance matsalar tsaro ta la’akari da wasu buƙatun makiyaya na musamman da kuma zaman lafiya na yau da kullum, musamman ma a yankunan da suke fama da tashe-tashe hankula da masu tsattsauran ra’ayi a yankunan makiyayan.

Domin ƙarn bayani, dubi: Wafula, Caleb Maikuma. *Makiyaya da Zaman Lafiya Yau da Kullum: Muhimman Hanyoyi da Darassu Domin Wanzar da Zaman Lafiya da Yayyafawa Rikici Ruwa daga Turkana ta Arewa a ƙasar Kenya*. Kungiyar RESOLVE, 2024.

# MUHIMMAN SAKAMAKON BINCIKE

**Duk da yake makiyaya a Turkana suna fuskantar matsaloli da ƙalubale da ke haddasa rikici, har wa yau** ana dama wa da su wajen ayyukan wanzar da zaman lafiya da magance rikici da ya daɗe yana addabar yankin.

**Mu’amala ta yau da kullum—da ta haɗa da saye da sayarwa, amfani da kayayyaki tare, kamar ruwa da wurin kiwo,** auratayya da ƙungiyoyi, da bukukuwan gargajiya—kowane daga ciki waɗannan abubuwan suna taimakawa wajen wanzar da zaman lafiya na yau da kullum a tsakanin makiyaya Turkana ta Arewa da al’ummomin da ke kewaye da su.

**Akwai wasu manyan ƙalubale wajen tabbatar da waɗannan ayyukan wanzar da zaman lafiya na yau da kullum. Yayin da ake samun** taimako daban-daban na gwamnati da na ƙungiyoyin agaji a wasu lokuta a cikin yankin, batutuwan da suka haɗa da fari, sauye-sauye a yanayi, da ci gaba da ayyukan yan fashin daji da masu tashintashina suna da tasiri sosai wajen samar da wanzuwar zaman lafiya.

**Maimakon kawai a yi tunanin al'ummomin makiyaya a matsayin wuraren da ba makawa za su fuskanci rikici, akwai** masu tsara manufofi da masu aiwatarwa suna da damar yi nazari, ƙididdigewa, da kuma nazarin albarkatun da al'ummomin suka riga suka dogara da su don hana ko rage rikici, da kuma yin la'akari da goyon bayan wadannan albarkatun da ake da su.

# SHAWARWARI GA MA’AIKATA DA MASU TSARA MANUFOFI

**Domin fahimtar al'ummomin makiyaya da yanayin rikice-rikice da tashe-tashen hankula da ke kewaye da** su, ya kamata ma’aikata da masu tsara manufofi da su mayar da hankali ƙwarai ga tushen wanzuwar zaman lafiya na yau da kullum a tsakanin makiyaya da kuma guje wa mayar da hankali ko tsara al'amurra kawai ta manhangar tsaro ko rikici kawai.

- Tattauna mahimmancin zamantakewa da dangantaka da walwala tsakanin makiyaya da al'ummomin da suke hulɗa tare da su, fahimtar tushen zaman lafiya na yau da kullum da abubuwan da za su iya taimakawa ko raunana su zai iya taimakawa wajen inganta hanyoyin haɗin gwiwa tare da al'ummomin makiyaya domin a gudu tare a tsira tare.

**Akwai dalilan da ke haddasa tashintashina.  Ma’aikata da masu tsara manufofi da ke magance tashin hankali** da ta'addanci a yankunan da al'ummomin makiyaya ke rayuwa dole ne su yi la'akari da matsalolin muhalli, al'adu, da siyasa na musamman da ke fuskantar al'ummomin makiyaya musamman, da mahimmancin dangantaka da haɗin kai na zamantakewa (da ya haɗa da alaƙa da haɗin kai) wanda zai ba da damar. su tallafa wa rayuwarsu da kuma kula da hanyoyin da ake bukata don kiwon dabbobi.

- Wannan yana da muhimmanci musamman idan aka yi la'akari da sauye-sauyen yanayi na gida wanda ke tasiri wurin kiwo da albarkatun ruwa ga dabbobi, wanda zai haifar da buƙatar tafiye-tafiye da kuma dangantaka makiyaya da maƙwabtansu domin samun kula da dabbobinsu.
- Ya kamata a duba hanyoyi da dabarun magance rikici da tashin hankali a tsanake sannan a guje wa haifar da wasu ƙalubale ga rayuwar yau da kullum da zaman lafiya a tsakanin al'ummomin makiyaya.
- Idan aka yi la'akari da yanayin tsaro na P/CVE da ƙoƙarin yaƙar ta'addanci, ƙarin kulawa domin fahimtar waɗannan tsare-tsaren zaman lafiya na yau da kullum da muhimmancin tasirinsa a kansu.

**Zato da ke nuna da cewa makiyayan sun kasance masu halin ko-in-kula ko tashin hankali ko** shiga cikin ayyukan tashin hankali ba su haifar da ɗa mai ido ba kuma sun kasa yin la'akari da gudummar wanzuwar zaman lafiya da membobin wadannan al'ummomi ke bayarwa a kawace rana.

- Don ƙarin ƙoƙarce-ƙoƙarce na ɗabi'a, sani, da kuma yunƙuri domin hanawa da magance ta'addancin da ke faruwa a yankunan da ke da yawan makiyaya, masu tsara manufofi da masu aiwatar da ayyuka ya kamata su guji yin abin da bai dace ba kuma sau da yawa suna nuna ƙyama game da yanayin makiyaya da makiyaya.
- Maimakon tunkarar al'ummomin makiyaya a matsayin masu lahani ko matsalar tsaro, ma’aikata da masu tsara manufofi ya kamata su yi la'akari da yuwuwar bangarorin haɗin gwiwa da al'ummomin makiyaya domin a tsayin daka don samar da wanzuwar zaman lafiya a ɗaukacin al'ummomin da suke gudanar da ayyukansu.

# KUNGIYAR RESOLVE

Ingantaccen Bincike | atsarinAyyukan e | Ingantacciyar Manufa A Kan Tsattsauran Tashin Hankali

www.resolvenet.org | @resolvenet

*Ra'ayoyin da aka bayyana a cikin wannan littafin na marubuta ne. Ba lallai ba ne su yi daidai da ra'ayoyin RESOLVE Network, amincewa da abokan haɗin gwiwa da ke ba da gudummawa ga samar da wannan ɗaba'ar, Cibiyar Aminci ta Amurka, ko kowace kungiya ta gwamnatin Amurka.*

RESOLVE tana zaune a Cibiyar Zaman Lafiya ta Amurka, tana ɗorawa a kan ayyukan Cibiyar na tsawon shekaru na shiga tsakanin al’ummomin da rikici ya shafa

RESOLVE na son gode wa Ofishin Hukumar Kula da Ci Gaban Kasashen Duniya (USAID)'s Ofishin Afirka don karimcin tallafin da take bayarwa ga wannan rahoto da kuma Hanyoyi da Dabarun Koyo Na Wanzar Da Zaman Lafiya na RESOLVE.